**Competitive Scramble is an Evil Ingenuity: Proceedings from the International Conference on the Biography and Songs of Alhaji Abubakar Kassu Zurmi in Heroic Poetry**
A Publication of the Department of Nigerian Languages, Sokoto State University, Sokoto



| ISBN 978-978-62480-5-9 (Print) | ISBN 978-978-62480-5-9 (Online)
**DOI:** https://doi.org/10.65760/kassu.i1.39 **Website:** www.ssu.edu.ng |**Issue 1** | **April 2025**|

# Tasirin Zuga a Wasu Waƙoƙin Maƙaɗa Kassu Zurmi

**Maimunatu Sulaiman,**
**Aisha Muhammad Agigi,**
**Bashar Abdullahi**

Department of Hausa Language, Zamfara College of Arts and Science(ZACAS)

**Corresponding Author Maimunatu Sulaiman** Maimunatusulaiman7@gmail.com
(+234)8032145373

**Tsakure**
*Waƙa ta baka ko rubutacciya, tamkar gyaɗa ce, sai an fasa akan san mai ƙwaya. Waƙoƙin ɓarayi da ake wa wani kallo na daban, su ma suna ɗauke da wani saƙo na musamman ta fuskar ankarar da jama'a irin dabarun da ɓarayi suke amfani da su wajen sata, domin jama'a su hankalta su kuma kiyaye. Wannan takarda da aka wa taken "Dabarun Sata a Waƙoƙin Ɓarayi na Kassu Zurmi: Koyar da Sata ko Ankararwa? Takarda ce da ta yi nazarin wasu waƙoƙin ɓarayi na Kassu Zurmi guda biyu, domin fito da saƙon da waƙoƙin suke ɗauke da su na ankarar da jama'a dabarun sata da ɓarayi suke amfani da su. An yi amfani da rubutattun bayanai da sauraron waƙoƙin mawaƙin domin fito da misalai. A ƙarshen an gano cewa akwai wasu lokuta da yanayi da ɓarayi suka fi so domin yin sata, wato kamar yanayi na damina da duhu, da kuma dare, sukan kuma yi sanɗa da dudduƙe domin kada motsin tafiyarsu ya tada mai gida.*

**Copyright:** *Provided that the author(s) and the source are credited, noncommercial use of the article is allowed, including printing and distribution.*

## 1.0 Gabatarwa

Waƙoƙin ɓarayi suna fama da ƙalubale na tuhume-tuhume da kallon haddarin kaji da ake musu, a saboda tunanin Hausawa na cewa waɗannan waƙoƙin ba wani saƙo da suke ɗauke da shi face koyar da sata, ko ƙarfafa wa ɓarayi gwiwa, da zuga su domin su yi sata. Sai dai wannan takarda tana son ta amsa irin wannan tuhume-tuhume na al'umma kan

***Tsakure***

*Zuga wasu kalamai ne da mawaƙi ke amfani da su don cicciɓa wanda yake yiwa waƙa da nuna fifikonsa kan wasu. Makaɗa Abubakar Kassu Zurmi sanannen mawaƙi ne a ƙasar Hausa. Wanda ya ƙware sosai wajen kiɗan Maza. Yana da hikima da fasaha da ke zuga wanda yake yiwa waƙa, Manufar wannan muƙala ita ce; Fito da wasu kalamai na zuga da makaɗa Abubakar Kassu Zurmi ya yi amfani da su cikin waƙoƙinsa.Bayyana tasirin waɗannan kalamai na zuga da yake yi domin gwarzanta wanda yake yi wa waƙar,bayyana matsayin waɗannan kalamai na zuga a al'adance.Za a yi amfani da hanyar fira da ma'abota ilimi musamman abin da ya shafi waƙar baka.Haka kuma za a yi amfani da hanyar sauraron wasu daga cikin waƙoƙin makaɗa Abubakar Kassu Zurmi domin samun hujjojin gina wannan muƙala.Ba wannan kaɗai ba,za a yi amfani da hanyar karance- karancen bugaggun littattafai da kundaye da mujallu da muƙalu da aka gabatar domin ƙara wa juna sani, duk domin samun hujjojin da za su gina wannan muƙala.hanyar ɗora aikin da aka yi amfani da ita kuwa ita ce;Mazhabar waƙar baka Bahaushiya.Sakamakon wannan bincike ya gano cewa mafi yawan waƙoƙin Makaɗa Abubakar Kassu Zurmi suna ƙunshe da zuga a cikinsu.Sannan nauyin wannan zugar yana tasiri ga zukatan waɗanda aka yi wa.A mizani na al'ada kuwa, ana danganta wannan zuga da kwarzanta wanda ake yi wa har ya yi wata bajinta ko jarumtakar da ba a zaton zai yi sai ya yi saboda zugar. Haka kuma yin wannan zugar yana nuna nauyin yadda makaɗin ke kallon jaruman da yake yi wa waƙar.*

**Muhimman Kalmomi:** Zuga, tasirinta, Waƙoƙin Kassu Zurmi.

## 1.1 Gabatarwa:

Kamar yadda aka sani, makaɗa Kassu Zurmi mawaƙin baka ne, wanda ya shahara fagen kiɗan maza.Yana da hikima ta tsara magana da yake koɗa mutum ko tawagar mutane a cikin waƙar,da kuma gwama wasu kalamai da za su cicciɓa mutum ko jama'a har ya/su yi wata shahararriyar bajinta. A cikin tubalan ginin waƙarsa yakan yi amfani da Zuga, wato wasu maganganu da yake faɗi ga wani mutum ko mutane waɗanda suke nuna fifikonsa/su kan wasu, waɗannan kalmomin za su zaburar da shi\su ya\su yi bajintar da za ta ba da mamaki matuƙa gaya.Lura da waɗannan hikimomi da yake da su ya ja ra'ayinmu matuƙa wajen fito da waɗannan kalamai na zuga da ya yi a cikin wasu waƙoƙinsa,domin kwarzanta wanda yake yi wa,da kuma nuna tasirin waɗannan kalamai ga zukatan waɗanda ya yi wa waƙar. da ma tasirinsu ga masu sauraro.

## 1.2 Ra'i ko Hanyoyin Ɗora Aiki:

Kalmar ra'i tana nufin wata tsararriyar hanya ta ilimi wadda wani masani ko manzarci ya tsara.Sannan aka ɗauke ta kan ci gaba dake tattare da ita.

Ra'in da za a ɗora wannan aiki a kansa shi ne Mazhabar Gusau(1993-2003 da 2011 da 2014 da 2015)ta nazarin waƙar baka Bahaushiya.

Ita wannan mazhabar waƙar baka Bahaushiya tafi raja'a ne da ba da ƙarfi wajen bayyana tarihi da asali da salsalar waƙar baka ta Hausa da zurfafa bayani kan turke da ayyana tubalin ginin turke da yananyin sassarƙuwar adabi da al'adar waƙar baka da nazarin awon baka da adon harshe dakuma  aiwatar da harshe. Mazhabar ta ƙunshi waɗannan da dabaru na farkon waƙar baka.

### 1.3 Taƙaitaccen Tarihin Abubakar Kassu Zurmi:

alhaji Kassu Zurmi wanda sunansa na yanka shi ne Abubakar, an haife shi a wani gari da ake kira magarya ta ƙasar Zurmi a jahar Zamfara ta yanzu. Sunan mahaifin Kassu Zurmi Muhammadu, mahaifyarsa kuwa Maimuna. Mahaifinsa Muhammadu Ganga kiɗan farauta ya yi, saboda haka ya yi gado ne ba da rana tsaka ya fara ba. Kassu Zurmi bai yi ilimin zamani ba, amma ya ɗan taɓa na Alƙur'ani. Tun kuwa lokacin da ya isa misalin mutum ne ya fara bin tsohonsa waje kiɗan farauta. Kassu Zurmi ya gaji mahaifinsa wajen kiɗan farauta. Abin da yake kaɗawa kuwa kalangu ne. Kassu Zurmi ya taɓa kiɗan noma.To amma da yake ya yi ne kawai don sha'awa bai mayar da hankali a wannan kiɗan ba. An ce "Gado girman ɗa"da yake kiɗan farauta Kassu ya gada sai ya mayar da hankali a kansa. Kiɗan farauta da kiɗan tauri su suka fito da shi fili har jama'a suka san shi sosai da sosai.duk wanda yasan Kassu Zurmi ya san shi ne a matsayin makaɗin maza.

A matsayinsa na makaɗin farauta ba wai gidajensu kawai yake bi idan ana suna ko biki ya kama ba,tare da shi ake  zuwa daji farautar.A cikin waƙar gagarau na magaji cewa ya yi:

Jagora:Tahiya madoka ko dajin kuna,<br>
:kowaj ji 'yan kalangaina na tahi an nan,<br>
:sai ɗa da ɗa ka kai naman daji.

Kafin rasuwarsa ya yi fiye da shekara ashirin rabonsa da zuwa wajen farauta. Amadu Kassu Zurmi ya shekara saba'in da huɗu zuwa da biyar a duniya ya bar 'ya'ya goma wasu daga cikinsu sun rasu bayan rasuwarsa.Yaransa da suka rage ba su ɗauki  wannan sabga tashi ba,sun bi hanyar makaranta ta koyar da sha'anin addinin musulunci.

### 2.0 Ma'anar Zuga:

zuga wasu kalmomi ne da ake amfani da su a koɗa wani mutum,a cicciɓa shi a nuna fifikonsa a kan wasu.Zuga wata magana ce,wadda mawaƙan Hausa na baka ko rubutacciya ke amfani da shi domin su ingiza ko harzuƙa wani mutum ya aikata wani abu wanda ba zai iya yinsa ba idan yana cikin hankalinsa.Wani lokacin kuma,zuga yana nufin kambama wani mutum ya ji cewa ba wani mutum da ya kai shi ƙarfi ko hazaƙa ko dukiya ko daraja ko kyauta a duniya.Zuga wata dabara ce da mawaƙan baka suke amfani da ita wajen harzuƙa jarumansu,wajen yin wata bajinta ta ban mamaki.

Mawaƙa suna cikin  sahun farko cikin jerin mazuga a ƙasar Hausa,wanda suna

yin wannan zuga tasu a cikin waƙoƙinsu,inda suke zuga gwanayensu ko  waɗanda suke yi wa waƙa.Cikin waɗannan mawaƙa waɗanda suka kasance tushen waƙoƙin baka a ƙasar

Hausa akwai Abubakar Amadu Kassu Zurmi,kuma shi ne za mu nazarci zuga a cikin wasu waƙoƙinsa.Wannan zuga ta kasu kasha uku kamar haka:

a.Zugar kariyar kai.

b.Zugar ingiza mai kantu ruwa.

c.

**2.1 Zuga a Wasu Waƙoƙin Abubakar Amadu Kassu Zurmi:**

Makaɗa Abubakar Kassu Zurmi,makaɗi ne mai hazaƙa da hikima waje sarrafa harshensa domin ya isar da saƙo ga masu sauraro cikin hanzari.Mawaƙin ya yi amfani da zuga cikin waƙoƙinsa domin ya kwarzanta gwanayensa su yi wata babbar jarumta kasancewarsa makaɗin maza.Ga misalai kamar haka:(Waƙar Ibrahim Shaho/Iro shaho)

Jagor : Gudunmawar kada sai masu
:Na jibir baban gajere,
:Mai gagara badau,
:Iro iyakar tauri,
:Daga kai sai ƙumba,ina wani
:Madadinka?na goje,
:Kai ko wakkai gareka ya kai iyakar tauri..........

A waɗannan ɗiyan waƙa zuga ce Kassu Zurmi yake yi ma shaho,inda yake kwatanta shi da kada,watau sai dai taron jama'a za su iya da shi ba dai ɗaiɗaikun 'yan tauri ba.Haka kuma ya kwatanta shi da wani shaharerren ɗan tauri da ba su yi zamani tare ba,tare da zuga shi cewa ya mafi wannan dan taurin daga shi, sai shi babu wani namiji a gabanshi,ya kuma ƙara cicciɓa darajarshi ta nuna mashi cewa duk wanda ya faɗa mashi tau ya kai iyakar tauri,watau ya kai karshen tauri kenan.Wanda a zahirin abun ba haka ba ne akwai mazaje a gaban shaho zuga ce kawai yake yi masa a matsayinsa na gwarzonsa.kuma wannan zugar ta yi tasiri sosai ga Shaho,dama masu sauraoro don ba don tahiri ba za a ɗauka haka abun yake.Haka kuma ya ƙara fito da zuga a wata waƙar tashi kamar haka;

(Waƙar Nagidan Duwa)

**Jagora** :Ina jikan Bawa buzun kura,
:Mai dabo gajere mazaizan duniya,
:Jan zaki nagidan duwa,
:Gajere mazaizan duniya,
: Mai dabo sabtun doki kahi mantuwa,
: Yaro ƙarya ya kai,
: Jama,a kun ji kiɗin nagidan duwa,
: Wani ɗan tcwaga mai tsaurin ido.........

A waɗannan ɗiyan waƙa Kassu Zurmi ya yi zuga ne ga wani ɗan tauri Nagidan Duwa,inda ya yi masa zuga tare da kwatanta shi da buzun kura,ya kuma ƙara kwatantashi da sautun doki mai wuyar mancewa.Wato yana son ya bayyanawa masu sauraro cewa ba zai yiwu

a iya mancewa da shi ba saboda jarumtarsa a fagen tauri da farauta.Wannan kirari da Kassu ya yi ga wannan jarumi ya nuna cewa jarumin gwanin Kassu ne a wannan sabga kuma yana ji da shi matuƙa gaya.Haka kuma ya cicciɓa shi gaban abokan gabansa,hakan kuma yakan ƙarawa jarumi kwarjini da muhibba ga idon masu kallo da sauraro.Ya kuma kwatanta shi da jan zaki,domin jan zaki ya ɗaramma sauran zakuna kwarjini da ƙarfi,anan,Kassu Zurmi yana bayyana gwaninsa da babban gwarzo cikin gwaraza,wato ko cikin jarumai shi babba ne,ya kuma zuga shi da cewa ga shi ɗan karami sai tsaurin ido,duk da zaman shi ɗan tsurut a halitta baya da tsoro ko kaɗan.aWannan zuga ce babba ya yi ga nagidan duwa kuma ta yi tasiri gare shi don ya yi abun da ya kamata a lokacinsa.Ga wani misalin kamar haka (Waƙar isa Ɗan buzu)

**Jagora** :

:Dodo na Audu ba ka da wa sai ƙane,
:Isah ɗan buzu,
:Sugugum ɗaka ba sallama,
:Yi sannu da kura,
:Mai bin dare yi sannu da ƙwarin ƙasa,
:Kai ne ba su ba ne mai kora mai kamawa,
:Isah Ɗan buzu,
:Kaholamin dare sa karnai ciri,
:Bari mu zo da Isa mu yi mai kiɗi,
:Yanzu tun da hwara shigewa duhu,
:Nasan iya ɓarna ka kai,
:Kwasau jikan kwasau,
:Jama'a ɓarna cikin dare sai kura,
:Zaki cikin dare yaka ɓanna.

Wannan zuga ne da makaɗa Abubakar Kassu Zurmi ya yi ga jaruminsa inda yake kwarzanta shi tare da ɗaga darajarsa a kan abokan sabgarsa,inda yake kwatanta shi da jarumtar ba ya da wa sai ƙane,wato ya shiga gaban kowane mutum da suke sabgar tare da shi ,sai dai a bi bayansa.Haka kuma ya ƙara siffanta shi da dodo wato ya zama abun tsoro cikin mutanensa ya zama gagara badau kenan.Ya kuma ƙara yi masa,Zuga ta hanyar kwatantashi da shi ɗin dai ne ba su ba ne,shi ne mai korawa da kamawa duk shi kaɗai,saboda jarumtarsa.Wannan zuga ta yi tasiri ga wanda aka yiwa da kuma masu sauraro.Ya kuma ƙara zuga shi da nuna cewa sana'ar tasa ta sata gadonta ya yi ta hanyar kiransa kwasau jikan kwasau.Ya kuma kwatanta shi da ƙaholamin dare wato duk dare ba shi tsoronsa zai fita hulɗarsa,ya kuma kira shi da kura mai ɓarna cikin dare,da kuma kwatanta shi da zaki,ya bayyana cewa ya yi nisa ga wannan sabga ta shi.Ya kuma kira shi da kura cikin dare kika ɓanna,kasancewa sana'ar wannan jarumi shi ne sata,sai cikin dare ake yinta,kwatanta shi da kura da zagi zuga ce.Wannan zuga ce cikakkiya ya yi ga wannan jarumi wanda hakan ya tasirantu gare shi da kuma masu sauraronsa.Ga wani misalin kamar haka;

(Waƙar Nomau na Magarya)

**Jagora** :Habaa nomau,

:Nomau tushen hwaɗa karen masu gari,

:Nomau ko baka jin batun masu gari,

:Gauɗe baka matanki,

:Baba kaɗe baka baka,

:Nomau na magaji ƙanƙari ko Allahu na ruwa baka jiƙa,

:Wandara ko baka jin batun masu gari,

:Banawa kyawon hwaɗa ayo accakwama

:Baba akwaɓata baƙiƙirin ta kare maku can,

: Na magaji inga har magabata na hawa za a biɗa.

:Torankawan tsiya uban mai rogo,

:Ko fatara tay yi yawa takan zama iko,

:Nomau ko baka jin batun masu gari,

:Kibau cikon kwari na magarya,

: Audu baka yada tukurhwa ba,

:Baka yada taimakon yaƙi ba,

:Bunu Ko kuɗin gari asha hwa su hita.

Wannan zuga ne da Makaɗa Kassu Zurmi ya yi ga jaruminsa Nomau na Magarya,inda yake zuga shi da tushen faɗa ne shi,wato shi ne asalin faɗa,kuma ya ƙara zuga shi da shi ne ƙarshen tsiya ba wata moriya a tattare da shi,ya kuma kwatanta shi da Gauɗe baka matanki,wato ba a more mashi don tsiya,ya kuma zuga shi da kaɗe baka baka,zugar na nuna don zamanshi ƙarshen tsiya da faɗa duk inda aka taɓo shi ba za a iya samun komai ba na amfani.Haka Kassu ya ƙara zuga shi da torankawan jiya,ya kuma kira shi da ko Allahu na ruwa baya jiƙa,ya kwatantashi da fatarar ta shi har ta zama iko.Ya kuma zuga shi da kibau cikon kwari wato ya zama faɗa baya cika sai da nomau na magarya.Kassu bai gushe ba yana ƙara zuga shi da bai yada yin tukurhwa ba.Tukurhwa shi ne ajon da manoma ke yi lokacin kaka idan an kai ga abun noma,sai atattara a kai gidan mai gari.Ya kuma zuga shi da bai yada taimakon yaƙi ba,sai ya ce bunu ya lallaɓa shi a samu ko kudin jangali a samu a amsa gare shi.Wannan zuga da Kassu ya yi ga wannan jarumin nasa ta yi tasiri gare shi sosai don ta saka mashi iko da ɗagawa duk da tsiyar da yake tattare da ita.Haka wannan zuga ta yi tasiri ga masu sauraro don ta ɗaga martabar wannan Ɗantaurin duk da tsiyar da yake fama da ita.Ga wani misalin wata waƙar kamar haka; (waƙar ɓarawo Garba)

**Jagora** :Ya gagari gaba karen Galadima,
:Namagaji Garba kura mai aci wawai,
:Annan sada magaji Ɗangizgo na Ɗangido,
:Barkak ka da gaba.

A wannan ɗiyan waƙa zuga ce Kassu Zurmi ya yi ga wani jaruminsa mai suna Garba magamin mai tarko kaura namoda.Ya zuga shi da cewa ya gagari gaba wato babu wani da zai kawo mashi wargi cikin sabgarsa ta sata,ya kuma ƙara zuga shi da kura mai aci wawai,wato anan yana son ya bayyana mashi cewa duk yadda yake da mutum zi ya yi

mashi sata.Ga al'adar Hausawa idan aka kwatanta mutum da kura to tabbas ɓacin sunansa ba ƙarami ba ne,wannan zuga ta yi tasiri matuƙa gaya ga wannan ɓarawo Garba dama zukatan masu saurare.Haka dai ya ci gaba da yin zuga a cikin wannan waƙa ta shi;

(Waƙar shaho)

Jagora :Nagoje gizago,

:Iro nagoje gizago uban gada baka da sabo,

:Ka ji annasarar yaƙi,

:Gobir ba jin kunya,

:Ka ji na bello yaba............

:Bari dai a baku rancen tsaba ku mai da soshiya don gayya,

:Shaho baban gajere ban barku gudu daji ba,

:Azara'ilu maganin wanda ka sheɗa duk,

:Iro jikan geshe maganin dum matsuraci,

:Allah bam man uban gada mai hana gayya,

:Gudummawar kada sai masu,

: Nagoje ƙarya ce ba a jema giwa da asuta.

A waɗannan ɗiyan waƙa zuga ce Kassu Zurmi ya yi ga Ibrahim Shaho,inda ya zuga shi da ba shi da sabo wato duk yanda yake da kai ta haɗa ku baya da sabo,ya kuma kwatanta shi da annasarar yaƙi,saboda yana jin cewa ya kware a fagen faɗa,ya kuma zuga shi ta hanya kwatanta shi da Azara'ilu mai ɗukar rai,wannan zuga ce da yake son ya nuna cewa duk wanda ya bkara da shaho sai dai wani ba shi ba don zai kashe shi.Ya ƙara kwatanta shi da maganin duk matsuraci,wato duk wani marar kuya yana maganinsa.Harwayau,bai gushe ba yana ƙara zuga shi da ɗaiɗaikun mutane ba su iyawa sai dai gayya ko gayyar sai sun shirya sosai.Kassu ya ƙara zuga shi da cewa shi giwa ne ba a zo mashi da ƙananan kayan faɗa don ya gagare su.Wannan zuga da Kassu Zurmi ya yi ga wannan jarumin na shi ta kai zuga don ta yi tasiri gare shi ya yi jarumtar da ta kamace shi, ta kuma yi tasiri ga zukatan masu sauraro.Ga wani misalin kamar haka;

(Waƙar Ɗantauri Labbo na Amadu Jabanda)

**Jagora**:

:Gagarau na Muhamman,
:To!
:Na Amadu Labbo mahaukata na magaji,
:An bak kaima sakkwato gaba,

:Ba a zuwa hwaɗa jabanda,
:Kowac ce za shi kaa a hana shi,
:Ɗan nema kubash shi a horai,
:Na hwaɗa maku jabanda ɗan daji ce,
: Amma hwa ta ci birane,
:Ba dai wagga 'yar shiya ba,
:Sai jangeru tayo gayya,
:Jangerawa iyalan ƙumba,
:Kila a tarbi shanun Gandau,
:Masu kiyon mutum da takobi.
:Ban dai hana yaro hawan kuka ba,
:Na Amadu amma hwa ya ɓantale takalmi,
:Hayaƙi tuƙaƙau,
:Tilas kuka hidda na kogo,
:Jabanda hurunhuruma maganin masu kaya,
: Kiris ɓata kayan jakki,
:Ruwan dare ɓata kayan jaki ya ɗora hwaɗi,
: Don ba gari nai ne ba,
:Namagaji ruwan zahi magani mai zwari,

: Ko dai an gunɗe ku ba a haɗe ku.

Wannan zuga ce da Kassu Zurmi ya yi ga Ɗauntauri Labbo Na Amadu Jabanda inda yake zuga shi tare da zuga garinsu jabanda.Kassu Zurmi ya zuga wannan ɗan tauri inda ya zuga shi da gagarau wato ya gagari duk wani abokin sabgar tasa,ya kuma zuga shi da mahaukata saboda illar da yake yi ga abokan gaba tafi gaban hankali.A ɓangare guda kuma ya zuga garin da wannan ɗantauri ya fito wato jabanda.Inda ya ce ba a zuwa hwaɗa garin,ya kuma zuga garin da ƙaramin gari ne, amma kuma ya ci birare saboda jarumtarsu.Ba duk wata tawaga ƙarama za ta iya faɗa masu ba sai an yi gayyar jama'a.Haka dai ya yi ta zuga wannan jarumin da kuma garinsu jabanda,ya kuma zuga shi da cewa ruwan zafi ne shi maganin mai zwari.Wato ko an faɗa mashi ba a yi nasara kan shi.Wannan zuga da Kassu ya yi gare shi da garinsu ta yi tasiri sosai don ta ɗaukaka darajarsa da kuma darajar garinsu jabanda.

## 2.2 Sakamakon Bincike

Wannan muƙala ta gano cewa Zuga dabara ce da Abubakar Kassu Zurmi yake amfani da ita wajen kwarzanta mazajen da yake yiwa waƙa domin su yi bajintar ban mamaki.Kassu yana amfani da zuwar ingiza mai kantu ruwa wajen cicciɓa darajarsu tare da ƙasƙanta

abokan gabansu.Haka kuma, muƙalar ta gano cewa mafi yawan waƙoƙin Kassu Zurmi suna ɗauke da zuga a cikinsu.Wannan zuga kuma tana matuƙar yin tasiri ga zukatan waɗanda yake yiwa zugar da kuma zukatan waɗanda ke saurare.

## 2.3 Kammalawa

Hausawa kan ce"komai nesan jifa ƙasa zai faɗo"kuma komai nisan dare gari zai waye.Wannan takarda a nan ta kawo ƙarshe,a wannan takarda an yi magana ne a kan zuga a wasu waƙoƙin makaɗa Abubakar Amadu Kassu Zurmi.An kawo taƙaitaccen tarihin mawaƙin musamman abun da ya shafi haihuwarsa da ƙuruciyarsa,da fara waƙarsa.Kuma an yi bayanin hanyoyin da aka bi wajen tattaro bayanai.A takardar, an kawo ma'anar zuga daga wasu masana daban-daban suka kawo.Sannan an kawo misalan wasu ɗiyan waƙoƙin Kassu Zurmi,waɗanda ke ɗauke da nau'o'in zuga daban-daban,dama nau'in zuwar da yafi amfani da ita ga jarumansa,tare da yin sharhi gwargwadon fahimta.An gano cewa Abubakar Amadu Kassu.Kassu ya ƙware wajen zuga 'yan tauri da ɓarayi ta hanyar kwatanta su da wasu manyan jaruman halittun dawa,tare da cicciɓa su tare da kambamasu fiye da asalin jarumtar tasu ta asali.Hakan yakan yi tasiri sosai da sosai a zukatansu,dama zukatan masu kallo da masu sauraro.A taƙaice waɗannan nau'o'in zuga da Kassu Zurmi ke yi a cikin zubin waƙoƙinsa suna ƙara ɗaukaka darajar waɗanda ake yiwa,kuma suna tasiri ga waɗanda ake yi wa dama masu sauraro.

## Manazarta


Aminu I.da wasu(2024)yabo a wasu waƙoƙin Makaɗa Sa'idu Faru: Takardar da aka gabatar a taron ƙasa da ƙasa kan rayuwa da waƙoƙin Makaɗa Sa'idu Faru.

Ahmad M.(2016)Kassu Zurmi da waƙoƙinsa:Spectrum Books ltd,Ibadan.

Bagari D.(1986)Bayani Hausa,jagora ga mai koyon ilimin harshe:Rabat-moroc, Imeremerie El-Maarif Al-jadida.

Gusau,S.M(2015)Mazhabobin Ra'i da tarken adabi da al'adun Hausawa:Century Research and publishing limited.

Ibrahim Baba da wasu(Masters in view)Nazarin salon zuga a wasu waƙoƙin Ibrahim Narambaɗa Tubali:P0stgraduate students,Bauchi State,university Gaɗau,Bauchi.

Yasira H.da wasu(2024)Tarken yabo ga zuga a cikin wasu waƙoƙin Sa,idu Faru Takardar da aka gabatar a taron ƙasa da ƙasa kan rayuwa da waƙoƙin Sa'idu Faru wanda jami'ar gwamnatin tarayya ta shirya,Gusau jahar Zamfara.

Yahya,A.B.(1997)Jigon nazarin waƙa.Fisbas media service,Kaduna